تِلاوت کی فَضِیلت

# FALALAR KARATUN AL-QUR’ANI MAI GIRMA



Shaykh-e-Tariqat, Ameer-e-Ahl-e-Sunnat
Founder of Dawat-e-Islami, Allamah Maulana Abu Bilal
**MUHAMMAD ILYAS**
Attar Qadiri Razavi

تِلاوت کی فضیلت

Falalat-Tilawa

# FALALAR KARATUN
# AL-QUR'ANI MAI GIRMA

Majlis Al-Madina-tul-Ilmiyya ya gabatar da wannan littafin da harshen Urdu. Wanda **Sashenan mai kula da fassara na Dawat-e-Islami** ya fassara shi izuwa harshen Hausa. Idan kun sami kuskure a cikin Fassarar ko abun da littafin ya kunsa, da fatan za a yi kokarin sanadda sashen fassara (department de traduction) a adresin na akwatin sakonni, lambar waya ko imel mai zuwa, don samun lada mai yawa.


**Département de traduction (Dawat-e-Islami)**

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagran, Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan

**UAN :** ☎ +92-21-111-25-26-92 – Poste. 7213

**E-mail:** 🖃 french.translation@dawateislami.net

**Falalar Karatun Al-Qur'ani Mai Girma**

Fassara harshen Hausa ta « Tilawat ki fazeelat »

✄

**DUKKAN HAKKOKIN MALLAKA**

Copyright © 2025 Maktaba-tul-Madinah

---

Ba a yadda ba sake wallafa ko watsa wani ɓangare na wannan littafin ta kowace hanya, ko tsari ko ta wani ha'li, na'ura, kwafi, rikodi ko waninsa, ba tare da rubutaccen izinin Maktaba-tul-Madinah ba.

---

| | |
|---|---|
| **Bugu na farko :** | Sha'ban-ul-Murajjab, 1446, AH – (Feb 2025) |
| **Edita :** | Maktaba-tul-Madinah |
| **Quantité :** | - |
| **ISBN :** | - |

## DAUKAR NAUYI

Kada ku yi wata-wata, ku tuntuɓemu kai tsaye don daukar nauyin buga wani littafi addini domin aika ladan ga yan uwanku mamata ta wadannan hanyoyi :

**Maktaba-tul-Madinah**

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah Mahallah Saudagran,
Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan

✍**E-mail :** global@maktabatulmadinah.com | feedback@maktabatulmadinah.com
✆ **Téléphone:** +92-21-34921389-93
💻**Web:** www.dawateislami.net | www.maktabatulmadinah.com

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ وَ الصَّلٰوةُ وَ السَّلَامُ عَلٰى خَاتَمِ النَّبِيّٖنَ

اَمَّا بَعْدُ فَاَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ ؕ بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ ؕ

## Addu'ar karanta littafi

Ku karanta Addu’ar nan kahin fara karatun littafin addini Musulunci, ko kuma wani darasi na musulumci, za ku tuna duk abunda kuka karanta اِنْ شَآءَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ:

اَللّٰهُمَّ افْتَحْ عَلَيْنَا حِكْمَتَكَ وَانْشُرْ
عَلَيْنَا رَحْمَتَكَ يَا ذَاالْجَلَالِ وَالْاِكْرَام

## FASSARA ADDU’AR

Ya Allah عَزَّوَجَلَّ ! Ka buɗa mana kofofin ilimi da hikimar ka, ka lulluɓemu da rahamar ka, ya ma’abuci daukaka da girma !

*(Al-Mustatraf, juzu’i na 1, shafi na 40)*

**Karin bayani:** ku yima Annabi ﷺ salati kafin kuyi addu'a da bayan kun idar da addu’a.



www.dawateislami.net

# Abubuwan da littafin ya kunsa


falala Da Nagartar Karatun Al-Qur'ani Mai Girma

falala Da Nagartar Karatun Al-Qur'ani Mai Girma ....................1

Falala Salāti-ga-Annabi ﷺ ....................1

Girman Masoyin Al-Qur'ani mai Girma ....................2

Harafi guda na da lada goma ....................3

Mafi alkhairin mutum ....................3

Al-Qur'ani ya na ceto kuma yaja mutun izuwa Aljannah ....................4

Falalar koyar da aya guda ko sunna Annabi guda daya ....................5

Sakamako mai yawa har izuwa ranar kiyama ga wanda ya koyar da aya guda daya ....................5

Allah عَزَّوَجَلَّ yana lullumka ladar har sai kiyama ta tashi ....................6

Ya hardace rabin Al-Qur'ni (juzu'i 15) a cikin-cikin mahaifiyarsa ....................6

Lu'a lu'an Madina 21 dangane da karatun Al-Qur'ani mai Girma ....................8

Yaro ya bayyan abinda ke ɓoye (ya tona asiri) .................... 12

Wajibi ne ga dukkanin musulmi ya karanta Al-Qur'ani daidai kuma ya bar bata karatun Al-Qur'ani mai Girma .................... 14

Nagartar karatun Al-Qur'ani na yara .................... 15

Lu’a lu’an Madina 14 game da Sujudin Tilâwat.......................... 16
Domin biyan bukatu..................................................................... 19
Ayoyin 14 wanda ake sujudi a gurin su......................................... 19
Lu’a lu’an Madina 9 gameda taba Al-Qur’ani mai Girma......... 22
Madani Bukata mahimmiya ga Mawallafa .................................. 24
Lu’a lu’an Madina 4 gameda Fassara Al-Qur’ani mai Girma.... 25
Lu’a lu’an Madina 2 a kan binnewa ko nitsawa cikin ruwa na shafukkan Alqur’ani ................................................................... 27
Lu’a lu’an Madina 8 daban-daban ................................................ 29
Lu’a lu’an Madina 5 game da aika lada ga mamaci (Îsâl-e-Sawâb)......................................................................... 31
Hanyar aika lada ga mamaci (Îsâl-e-Šawâb)................................ 32
Hanyar karatun Fâtihaĥ............................................................... 32
Hanyar yin addou'a ta sadaka ga marigaya [Îsâl-e-Šawâb].......... 37
Lu’a lu’an Madina 17 dangane da Sunna ɗarma Rawani........... 38
Transliteration Chart.................................................................... 42



www.dawateislami.net

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ وَ الصَّلٰوةُ وَ السَّلَامُ عَلٰى خَاتَمِ النَّبِيّٖنَ

اَمَّا بَعْدُ فَاَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ

## FALALA DA NAGARTAR KARATUN

# AL-QUR'ANI MAI GIRMA

Duk yunkurin shaiɗan na ganin sai ya hana ku karanta wanna littafin, to kuyi kokarin karanta shi gaba ɗaya domin, اِنْ شَآءَالله za ku ci karo da tarin bayanai da ilimi mai kima.

### Falala Salāti-ga-Annabi ﷺ

Manzon Allah mafi karamci da kyautatawa kuma mafi so-yuwa a gremu (صَلَّی اللّٰہُ عَلَیۡہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم) ya ce : « Yin Salati a greni haskene akan sirāɗi. Duk wanda ya yimin Salati 80 a ranar Juma'a, za a gafarta masa zunumban shi na shekara 80. *(Al-Mu'jam-us-Saghîr, shafi na 320, Hadisi na 5191)*

*Yeĥī ĥay ārzū ta'līm-e-Quran ām ĥo jāey*
*Ĥar aik parcham say ouncha parcham-e-Islam ĥo jāey*

*Fatana Allah ya bunka'sa karatun AlQur'ani mai girma*
*Ya ɗaukaka tutar musulunci akan sauran tutoti*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Girman Masoyin Al-Qur’ani mai Girma

Sayyidunâ Shaykh Sâbit Bunânî قُدِّسَ سِرُّهُ النُّوْرَانِي ya kasance yana gama karatun AlQur'ani mai tsarki a kullum. Ya kasance yana azumi da rana, yana kuma yin nafila a cikin dare. Ya kasance yana yin Raka'a 2 na sallar nafila a kowane masallacin da ya wuce (wannan sallar ana kiranta da Tahiyya-tul-masjid). Yayin da yake faɗar albarka da ya samu, ya ce: “Na gama karanta Al-Qur’ani mai girma gaba ɗaya, na yi kuka a farfajiyar Uban-gijina a kusa da kowane ginshikan Masallacin Juma’a”. Yana da رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه tsananin son Salla da karatun Alqur'ani mai girma, kuma ana kwadayin samun albarkar mai yawa albarkacinsa. Saboda haka, bayan mutuwarsa, a lokacin binnewa wani bulo ba zato ba tsammani ya faɗa cikin kabari. Yayin da wasu suka sunkuyar da kansu domin dauko ta, sai suka yi mamakin ganin Shaihin رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه yana tsaye a cikin kabarinsa yana salla! Lokacin da aka tambayi ’yan uwansa game da hakan, sai ’yarsa mai daraja ta ce: “Babana mai girma رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه ya kasance yana yin wannan addu’a kowace rana: “Ya Allah! Idan Ka ba wa kowa falala na yin sallah a cikin kabarinsa a bayan mutuwarsa, to, ka yi mini ni'ima [irin wannan falala].

An ruwaito cewa, a duk lokacin da mutane suka wuce kabarin Shaihin mai albarka رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه, sai su rika jin karatun kur’ani mai tsarki daga cikin kabarin na sa mai albarka. *(Ḥilya-tul-Awliyā, juzu'i na 2, shafi na 362-366)*

Allah عَزَّوَجَلَّ Ya jiqansa, Ya gafarta mana ta hanyarsa.

اٰمِيْن بِجَاهِ النَّبِيِّ الْاَمِيْن صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم

## Harafi guda na da lada goma

Alqur'ani mai girma da daukaka maganar Allah عَزَّوَجَلَّ ce mai tsarki. Karatun Al-Qur'ani da karantar da shi da saurarensa da karanta shi domin wasu su saurare shi duk ayyuka ne na lada. Ta hanyar karanta harafi daga Alkur'ani mai girma, mutum yana samun lada goma. Dangane da haka Manzon صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce: “Wanda ya karanta harafi daga littafin Allah, zai samu wata falala wadda ta yi daidai da lada guda goma. Ba ina cewa الٓمّٓ (Alif-Lâm-Mîm) harafi ne ba, hasali ma اَلِف (Alif) harafi ne, لَام (Lâm) harafi ne, مِيْم (Mîm) harafi ne.” *(Sunan-ut-Tirmizi, juzu'i na 4, shafi na 417, Hadisi na 2919).*

*Tilāwat kī taufīq day day Yā Ilāĥī*
*Gunāĥaun kī ĥo dūr dil say siyāĥī*

*Ka bani ikon karatun Alqur'ani Ya Allah*
*Ya Allah Ka yaye mun Duhun Zunuban Zuciyata*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب　　صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Mafi alkhairin mutum

Mafificin mutum Fiyayyen halitta, Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce : "خَيْرُكُمْ مَنْ تَعَلَّمَ الْقُرْاٰنَ وَعَلَّمَه". Ma’anar hadisin shine : "Mafi alherin mutum a cikinku shi ne wanda ya koyi Al-Qur'ani mai girma, kuma ya karantar da shi ga wasu.” *(Sahîh Bukhârî, juzu’i na 3, shafi na 410, Hadisi 5027)*

Sayyidunâ Abû 'Abdur Rahmân Sulamî رَضِیَ اللهُ عَنْهُ ya kasance yana karantar da Alkur'ani mai girma a cikin masallaci sai ya ce : "Wannan hadisi ya sanya ni zama a nan. *(Fayd-ul-Qadîr, juzu'i na 3, shafi na 618, Hadisi na 3983)*

*Allah mujĥay Ḥāfiẓ-e-Quran banā day*

*Quran kay aḥkām pay bĥī mujĥ ko chalā day*

*Ya Allah! Ka sani inzamo Hafizin Alqur'ani Mai Girma*
*Ka tabbata dani in kasance mai kiyaye dokokin Alqur'ani mai girma.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Al-Qur'ani ya na ceto kuma yaja mutun izuwa Aljannah

An ruwaito daga Sayyidunâ Anas (رَضِیَ اللهُ عَنْهُ) daga Annabin mu, zaman lafiyar zukatan mu, mai girma masoyin mu صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce : « Duk wanda yakoyi kuma yake karantar da Al-Qur'ani mai girma, sanan ya kiyaye dokokin dake cikin sa. Al-Qur'ani zai ceton shi a ranar kuma ya kaishi Aljannah ». *(Al-Mu'jam-ul-Kabîr, juzu'I na 10, shafi na 198, Hadisi na 10450, Târîkhe Dimashq, juzu'i na 41, shafi na 3)*

*Ilāĥī khūb day day shauq Quran kī tilāwat kā*

*Sharaf day Gumbad-e-Khazrā kay sāye mayn shaĥādat kā*

*Ya Allah! ka samini son karatun Al-Qur'ani kuma kasa nayi mutuwar shahada karkashin kumbar nan koriya, sa karshe na ya zama hakan.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Falalar koyar da aya guda ko sunna Annabi guda daya

An ruwaito daga Sayyidunâ Anas رَضِیَ اللهُ عَنْهُ duk wanda ya koyar da aya guda ko Sunnah ga wanin sa, Allah عَزَّوَجَلَّ zai tanada masa da saka-mako a ranar tashin qiyama. Irin saka-mako da babu wanda yafi shi."
*(Jam'-ul-Jawāmi', juzu'i na 7, shafi na 281, Hadisi na 22454)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Sakamako mai yawa har izuwa ranar kiyama ga wanda ya koyar da aya guda daya

An ruwaito daga ma' abucin haske guda biyu, wanda ya tattare Al-Qur'ani mai girma, Sayyidunâ 'Usmân Ibn 'Affân رَضِیَ اللهُ عَنْهُ daga Manzo Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce : "Duk wanda ya koyar da Aya Al-Qur'ani mai girma, ya na samun linkin lada fiye da wanda ya koyama [aya]." Cikin wani hadisin, an ruwaito daga Sayyidunâ Anas رَضِیَ اللهُ عَنْهُ cewa Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce : "Duk wanda ya koyar da aya guda ta Al-Qur'ani mai girma, ya na cigaba da samun ladansa, matukar ana karanta wanna ayar." *(Jam'-ul-Jawâmi', juzu'i na 7, shafi na 282, Hadisi 22455-22456)*

*Tilāwat kā jażbaĥ 'aṭā ker Ilāĥī*
*Mu'āf farmā mayrī ĥar khaṭā Ilāĥī*

Ya Allah ! ka samini son karatun Al-Qur'ani
Ya Allah ! ka gafarta muni zunubbai na da rahamarka

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Allah عَزَّوَجَلَّ yana lullumka ladar har sai kiyama ta tashi

Ya tabbata a cikin wani hadisi cewa : "Duk wanda ya koyar da aya daga littafin Allah عَزَّوَجَلَّ ko kuma wani babi na ilimin addini, Allah عَزَّوَجَلَّ zai cigaba da samun lada har ranar sakamako." *(Tārīkhe Dimashq, juzu'i na 59, shafi na 290)*

*'Aṭā ĥo shauq Maulā Madrasay mayn ānay jānay kā*
*Khudāyā żauq day Quran pařĥnay kā pařĥānay kā*

*Ya ubangiji na ! Ka samuni son karatu da neman ilimin addini*
*Ya Allah ! Ka bani himmar koyo da koyar da Al-Qur'ani mai Girma*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Ya hardace rabin Al-Qur'ni (juzu'i 15) a cikin-cikin mahaifiyarsa

Tambaya mai amfani, tare da amsarta mai haske, anan daga littafin Malfûzât-e-A'lâ Hadrat :

**Tambaya :** Mai martaba ! Shin akwai shekarun da shari'a ta kayyade na "Taqrib-e-Bismillah?"

**Amsa:** Babu wani abu da aka kayyade a cikin Shari'a [a kan haka], amma an yi la'akari da shekarun 4, watanni 4 da kwanaki 4. [Don haka] na malamai masu daraja. Lokacin da Sayyiduna Shaykh Khuwâjaĥ Qutb-ul-Haq Waddin Bakhtiyar Kâkî رَضِیَ اللهُ عَنْهُ ya cika shekara 4 da wata 4 da kwana 4 aka shirya 'Taqrīb-e-Bismillaĥ' kuma aka gayyaci mutane. Sayyidunâ Shaykh Khuwâjaĥ Gharîb Nawâz رَضِیَ اللهُ عَنْهُ

shima yana nan yana shirin tambayar yaron ya karanta بِسۡمِ الله, amma nan take aka yimasa ilhama [Ilĥâm] da : "Dakata, Hamîduddîn Nâgorî ya zo koyama [yaron karatun بِسۡمِ الله]". Daidai wannan lokacin a garin Nâgor, Qâdî Hamîduddîn رَحۡمَةُ اللّٰهِ عَلَيۡه akayimishi ilhama da yaje ya koyar da wani bawa cikin bayin Allah عَزَّوَجَلَّ karanta بِسۡمِ الله. Nan da nan, ya je bikin ya ce wa yaron : ''Ɗa na! Karanta "بِسۡمِ اللهِ الرَّحۡمٰنِ الرَّحِيۡمِ." Sai yaron ya fara karantawa "اَعُوۡذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيۡطٰنِ الرَّجِيۡمِ بِسۡمِ اللهِ الرَّحۡمٰنِ الرَّحِيۡمِ" kuma ya ci gaba da karantawa tun farkon Alqur'ani har ya gama karantawa Shaykh Qadi Hamīduddīn da Shaykh Khuwâjaĥ Gharîb Nawāz رَحِمَهُمَا اللّٰه ya ce: "Ɗana! Ci gaba da karantawa ! " Yaron ya amsa ya ce, "Na ji duk wannan a cikin mahaifiyata, kuma bakin abun da ta haddace, ni ma na haddace shi duka !" *(Malfûzât-e-A'lâ Hadrat, shafi na 481)*

Allah عَزَّوَجَلَّ yayi musu rahama kuma yaman gafara albarkacinsu.

اٰمِيۡن بِجَاهِ النَّبِيِّ الۡاَمِيۡن صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم

*Khudā Apnī ulfat mayn ṣādiq banā day*
*Mujĥay Mustafa kā Tū 'āshiq banā day*

*Ya Allah عَزَّوَجَلَّ! Fais que je sois sincère dans mon amour pour Toi*
*Et aussi fais de moi un fidèle sincère de Ton Prophète صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم!*

صَلُّوۡا عَلَى الۡحَبِيۡب      صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

Abin bakin cikin shi ne, saboda karancin ilimi a Musulunci, da yawa daga cikin Musulmi a yau ba su san hukunce-hukuncen Shari'a ba

dangane da karatun Alkur'ani, koyan Alkur'ani, sauraron Alkur'ani, yadda ake taba Al-Qur'ani da sauransu. Domin yada ilimin addinin musulunci, da nufin kubutar da musulmi daga zunubai, bayan haka sai a gabatar da wani fuloti mai launin lu'a lu'an madina.

## Lu'a lu'an Madina 21 dangane da karatun Al-Qur'ani mai Girma

1. Mai girma Amirul-Muminina, Sayyidunâ 'Umar Fârûq-e-A'zam رَضِیَ اللهُ عَنْهُ ya kasance yana sumbantar Alqur'ani kowace safiya, kuma ya ce: "Wannan shi ne alkawarin Ubangijina عَزَّوَجَلَّ da Littafinsa." *(Durr-e-Mukhtâr, juzu'i na 9, shafi na 634)*

2. Mustahabbi ne karanta Ta'awwuz "اَعُوْذُ بِاللهِ" a farkon karatun, kuma sunna ce karanta Tasmiya "بِسْمِ اللهِ" a farkon sura. In ba haka wato a farkon sura ba Mustahabbi ne. *(Baĥâr-e-Sharî'at, juzu'i na 1, sashe na 3, shafi na 550)*

3. Idan an fara karatun ne daga Suratul Tauba, sai a karanta Ta'awwuz da Tasmiya, amma idan aka fara karatun kafin wannan gurin kuma aka iso ga Suratul Taubaĥ a lokacin karatun, to ba sai a karanta Tasmiya ba. Karatun Ta'awwuz na musamman a farkon wannan sura, wanda wasu Huffaz na wancan zamani suke gabatarwa ba shi da tushe balle makama. Bugu da ƙari, akidar da tayyaɗu cewa bai kamata a karanta Tasmiyaĥ ba ko da farawa da karatun suratu At-Taubaĥ kuskure ne kawai. *(Ibid, shafi na 551)*

4. Mustahabbi ne karanta Alqur'ani da alwala, da fuskantar alqibla, da sanya tufafi masu tsafta. *(Ibid, shafi na 550)*

5. Karatun Alqur'ani mai girma a lokacin da ake kallonsa ya fi a karanta shi da ka, domin bai qunshi ba kawai karatun Alqur'ani mai girma, amma kuma kallonsa da taba shi, duk wadannan aykin ibada ne. *(Ghunya-tul-Mutamallî, shafi na 495)*

6. Sai a karanta Alkur'ani mai girma da sauti mai matukar kyau idan kuma mutum baida murya mai dadi, sai ya yi kokarin kawata muryarsa yayin da yake karantawa. Duk da haka, an haramta karantawa da sautin da ke haifar da kuskure, rashi ko ƙara haruffa, kamar yadda mawaƙa ke yi. A kula sosai don kiyaye qa'idodin karatun Al-Qur'ani [Tajwîd]. *(Durr-e-Mukhtâr, Rad-dul-Muhtâr, juzu'i na 9, shafi na 694)*

7. Yana da kyau a karanta Alqur'ani mai girma da murya mai sauti, matukar ba zai haifar da matsala ga masu sallah ba, marasa lafiya ko masu barci. *(Ghunya-tul-Mutamallî, shafi na 497)*

8. Yayin da ake karanto ayoyin kur'ani mai girma, wasu mutane duk da cewa sun yi shiru suna ci gaba da kallonsu suna ta motsi da motsi iri-iri. Ya kamata waɗannan mutane su lura cewa sauraren gameda maida hankali yana da mahimmanci ban dama yin shirun. Dangane da haka ne, shugaban Ahlul-Sunnah, Shaykh Imâm Ahmad Razâ Khân رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه ya ce a shafi na 352, juzu'i na 23 littafinsa Fatâwâ Razawiyyaĥ : "Wajibine a saurara da kyau kuma a yi shiru idan ana karatun Al-Qur'ani mai girma. Domin faɗar Allah عَزَّوَجَلَّ cewa:

وَ اِذَا قُرِئَ الْقُرْاٰنُ فَاسْتَمِعُوْا لَهٗ وَ اَنْصِتُوْا لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُوْنَ ﴿۲۰۴﴾

*"kuma idan an karanta Alqur'ani sai ku saurare shi, kuma ku yi shiru don ayi muku rahama."*

*[Kanz-ul-Îmân (Fassarar Al-Qur'ani)] (juzu'i na 9, Al-A'râf, Aya ta 204)*

9. Idan aka karanta Alqur'ani mai girma da babba murya, wajibine a kan dukkan mahalarta su saurare shi, matuqar sun taru domin sauraren sa. In ba haka ba, ya isa daya daga cikinsu ya saurare shi, yayin da sauran za su iya ci gaba da ayyukansu. *(Fatâwâ Razawiyyaĥ – référencé, juzu'i na 23, shafi na 353)*

10. Haramun ne ga kowane mutum a cikin taro ya karanta da babbar murya. A cikin taron Issāl-e-Sawab ga mamaci, yawanci kowa yana karantawa da babbar murya - wannan haramun ne. Idan mutane da yawa suna karantawa, qa'idar su ita ce su karanta da murya kas-kasa. *(Baĥâr-e-Sharî'at, juzu'i na 1, sashe na 2, shafi na 552)*

11. Idan ana karatu a masallaci wasu mutane suna nan suna salla ko addu'o'i, to sai ku karanta kasa-kasa ta yanda ku kadai ne ke iya ji. Ba tare da sauti ya isa ga mutumin da ke kusa da ku.

12. An haramta karatun kur'ani mai girma da babbar murya a kasuwa ko wurin da mutane ke aiki. *(Ghunya-tul-Mutamallî, shafi na 497)*

13. Haka kuma an haramta yin karatu da babbar murya a inda wani yake koyon ilimin addinin Musulunci, ko kuma inda dalibin ilimin addinin Musulunci yake bita ko yin bincike. *(Ibid)*



www.dawateislami.net

14. Babu laifi karatun Alqur'ani mai girma a kwance, matuqar an nade qafafu (wato ba a miqe su ba) ba a rufe fuska. Sannan kuma ya halatta a karanta yayin tafiya ko aiki, matukar zuciya bata shagaltu ba, idan ba haka ba ya zama Makruĥ [abin kyama]. *(Ibid, safi na 496)*

15. An haramta karatun Al-Qur'ani mai girma a bandaki ko a wuraren kazanta. *(Ibid)*

16. Saurаron karatun Alqur'ani ya fi yin karatun Alqur'ani ko yin sallar nafila. *(Ibid, shafi na 497)*

17. Idan wani ya karanta ba daidai ba, Wājib ne mai saurare ya gyara mishi, matukar hakan bai haifar da ƙiyayya ko hassada ba. *(Ibid, shafi na 498)*

18. Haka nan idan wani ya dauki AlQur'ani mai girma na wani dan lokaci, sai ya lura da kuskure wajen bugawa ko rubutawa, Wajib ne ya sanar da mai shi. *(Baĥâr-e-Sharî'at, juzu'i na 1, sashe na 3, shafi na 553)*

19. A lokacin rani yana da kyau a kammala karatun kur'ani mai tsarki da safe, yayin da lokacin sanyi ya fi kyau a kammala shi a farkon dare, domin ya zo a cikin Hadisi cewa: "Wanda ya kammala karatunsa. Na' Al-Qur'ani mai girma a farkon yini, Mala'iku za su nemi gafararsa har zuwa yamma, kuma wanda ya cika shi a farkon dare, Mala'iku za su nemi gafarar sa har zuwa safiya."



www.dawateislami.net

Kamar yanda a lokacin rani yini yafi dare tsayo, kammala karatun Al-Qur'ani mai girma da safiya zai sa a kara samun neman gafarar malaiku mai yawa. A daya bangaren kuma, darare sun fi tsayi a lokacin sanyi, don haka kammala karatun Al-Qur'ani mai girma farkon dare zai haifar da yawan (rokon) gafara. *(Ghunya-tul-Mutamallî, shafi na 496)*

20. Idan an kammala karatun Alqur'ani cikakke, yana da kyau a karanta Suratul Ikhlas sau 3. Wannan kuma ya shafi lokacin Sallar At-Taraweeh, amma idan aka gama a lokacin sallar farilla ne, kada a karanta surar Ikhlas fiye da sau daya. *(Ibid)*

21. Bayan kammala karatun Alqur'ani mai girma, bayan karanta suratun Nas, sai a karanta suratu Fatiha da Suratul Baqara har zuwa aya ta 5 وَ اُولٰٓىِٕكَ هُمُ الْمُفْلِحُوْنَ۝, sai a yi addu'a domin wannan Sunnah ce.

    Dangane da haka Sayyiduna Abdullahi bn Abbas رَضِیَ اللّٰہُ عَنْهُمَا ya ruwaito daga Sayyiduna Ubayyu Bin Ka'ab رَضِیَ اللّٰہُ عَنْہُ : " Lokacin da Manzon Allah صَلَّی اللّٰہُ عَلَیْہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم ya karanta "قُلْ اَعُوْذُ بِرَبِّ النَّاسِ۝", sai ya fara Suratul Fatiha, sannan sai suratu. Al-Baqarah har zuwa aya ta 5 وَ اُولٰٓىِٕكَ هُمُ الْمُفْلِحُوْنَ۝, bayan yayi addu'a ta kammala karatun Alqur'ani, sai ya dakata nan." *(Al-Itqân fî 'Ulûm-il-Quran, juzu'i na 1, shafi na 158)*

## Yaro ya bayyan abinda ke ɓoye (ya tona asiri)

Sayyidunâ Abû 'Abdullâĥ رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه ya ce: "Sayyidunâ Shaykh Abul

Hasan Muhammad Bin Aslam Tûsî عَلَيْهِ رَحْمَةُ اللّٰهِ الْقَوِى ya kasance yana ba da kulawa mafi girma wajen boye ayyukansa na alheri, har ya taba cewa: "Idan ya kasance a kaina, ina iyawa da na ɓuya daga Kirâman Katibina (mala'iku masu rubuta ayyuka) domin yin ibadar Allah عَزَّوَجَلَّ!" Mai riwayar ya ce: "Na shafe sama da shekara 20 a wajen Shaihin amma ban taba ganinsa ba, in ban da Juma'a, ya yi sallar nafila ko raka'a biyu. Shaikh رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه ya ɗauki tukunyar ruwa ya shiga cikin ɗakinsa na musamman sannan ya rufe ƙofar daga ciki. Ban taɓa iya sanin me yake yi a ɗakinsa ba sai watarana ɗan nasa ya fara kuka kworai. Yayin da mahaifiyar yaron ta fara ƙoƙarin kwantar masa da hankali, na tambayi ta: "Me ya sa yaron ya yi kuka haka?" Sai macen mai daraja ta ce: "Mahaifin wannan yaro (Sayyidunâ Shaykh Abul Hasan Tûsi رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه) yana karanta alqur'ani mai girma a cikin wannan daki yana kuka (dan tsoron Allah عَزَّوَجَلَّ), sai wannan yaron ma ya fara kuka yana jin kukan mahaifinsa!" Shaykh Abû 'Abdullâĥ رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه ya ce: "Shaykh Sayyidunâ Abul Hasan Tûsî رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه, domin ya kare kansa daga musiiba da ke tattare da riya, ya na yin taka-tsan-tsan wajen ɓoye ayyukansa na alheri, ta yadda bayan ya yi ibada a cikin dakinsa na musamman kafin ya fita sai ya wanke fuskarsa ya shafa ma idonsa kholli, ta yadda ba zai yiwu ba. Mutum ya yi tunanin cewa ya yi kuka ta hanyar kallon fuskarsa ko idanunsa ba!" *(Hilya-tul-Awliyâ, juzu'i na 9, shafi na 254)*

Allah عَزَّوَجَلَّ yaji ƙansa kuma yayi muna gafara don sa.

اٰمِیْن بِجَاہِ النَّبِیِّ الْاَمِیْن صَلَّی اللّٰہُ عَلَیْہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم

*Mayrā ĥar 'amal bas Tayray wāsiṭay ĥo*
*Ker ikhlāṣ aysā 'aṭā Yā Ilāĥī*

*Allah ka sa dukkanin aikina su zamo donka kawai !*
*Ka bani ihlassi, ina mai rokon ka ya Allah !*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب        صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

سُبْحٰنَ اللّٰـه عَزَّوَجَلَّ! A bangare guda kuma akwai waɗanda suka fi kowa gaskiya da tsoron Allah, suna boye ayyukansu na alheri, kuma abin takaici, a daya bangaren akwai masu butulci da raunin imani irinmu, muna kururuwa da bayyana dukkan ayyukan alherin da muke yi. Da farko dai, ba ma iya yin aikin alheri, idan kuma mukayi aikin alherin, sai mun bayyana shi!

*Nafs-e-badkār nay dil per yeĥ qiyāmat tawřī*
*'Amal-e-nayk kiyā bĥī to cĥupānay na diyā*

*Girman kai na ya taɓa mini cen-cikin zuciyata.*
*A duk lokacin da na yi aiki mai kyau, ba na iya boye shi.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب        صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Wajibi ne ga dukkanin musulmi ya karanta Al-Qur'ani daidai kuma ya bar bata karatun Al-Qur'ani mai Girma

Limamin Aĥl-Sunnat, 'Allâmaĥ Maulânâ Al-Hâj Al-Hâfiz Al-Qâdirî Shaiĥ Imâm Ahmad Razâ Khân رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه ya ce : "Ba shakka, koyan



www.dawateislami.net

isasshen Tajwîd don samun ikon furta kowane harafi daidai[1]. Kuma zaku kuɓutar da kanku, daga kuskuren karatun wanda yake farilla kaine [wajibine akan kowane musulmi]." *(Fatâwâ Razawiyyaĥ – référencé, juzu'i na 6, shafi na 343)*

## Nagartar karatun Al-Qur'ani na yara

Allah عَزَّوَجَلَّ idan yana son ya azabtar da mutanen duniya, amma idan ya ji yara suna karatun Alqur'ani sai ya kame da yi musu azabar. *(Sunan Dârimî, juzu'i na 2, shafi na 530, Hadisi na 3345)*

*Ĥo karam Allah ! Ḥāfiẓ Madanī munno kay ṭufayl*
*Jagmagātay Gumbad-e-Khazrā kī kirno kay ṭufayl*

*Ya Allah ! kabamu albarkar yaranda suka hardace AlQur'ani mai girma. Kayi muna albarka don kubbanan koriya, wanda haskenta ke kayatar da duniya.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب    صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

اَلْحَمْدُ لِلّٰه عَزَّوَجَلَّ! Daga dandalin Dawat-e-Islami - kungiyar fafutikar yada alkur'ani da Sunna ta kasa da kasa wanda ba ta siyasa - ta samar da (kafa) madrassa ba adadi a kasashe daban-daban na duniya, karkashin sunan Madrasa-tul-Madînaĥ. A yayin da muke rubuta wadannan

[1] Wato shi ne furta kowane harafi na AlQur'ani mai girma daidai mafitar sa bisa qa'ida ta Tajwîd.



www.dawateislami.net

layukan, a kasar Pakistan, yara maza da mata 50,000 ne ke koyon karatun kur'ani da haddar kur'ani kyauta a wadannan Aji. Bugu da kari, an kafa darussa ga manya masu son koyon ingantattun lafuzzan AlQur'ani mai girma da sunan Madrasa-tul-Madînaĥ (na manya) a masallatai da sauran wurare marasa adadi. A cikin wadannan darussa, masu shagaltuwa da rana da ayyukansu da sauran ayyukansu suna koyon yadda ake karatun AlQur'ani mai tsarki da addu'o'i da sunna daban-daban gaba daya da yamma na tsawon mintuna 40 bayan sallar isha'i. اَلْحَمْدُ لِلّٰه عَزَّوَجَلَّ! Irin wadannan cibiyoyi, masu suna iri daya, an kuma kafa su ga 'yan'uwa mata a Musulunci.

## Lu'a lu'an Madina 14 game da Sujudin Tilâwat

1. Sujudin Tilawat tana zama Wajibine idan mutum ya karanta ko ya ji an karata aya ta Sajdaĥ [sujjada]. *(Al-Ĥidâyaĥ, juzu'i na 1, shafi na 78)*

2. Karanta fassarar ayar Sajdaĥ a cikin harshen Farisa ko wani yare yana mayar da Sujjadaĥ Wajibi ga mai karatu da mai sauraro, shi mai sauraro ana fahimtar dashi cewa Aya ce ta Sujjdaĥ ko kuwa ba ta Sujjadh bace. Sai dai wajibine a sanar da shi cewa fassarar ayar Sujjdaĥ ce a ka karanta, idan bai sani ba. Idan kuma ya kasance karatun Aya ne ta Sujjdaĥ, to babu buqatar sanar da mai saurare cewa aya ce ta Sujjadaĥ. *(Fatâwâ 'Âlamgîrî, juzu'i na 1, shafi na 133)*

3. Sharadin karatun shi ne, muryar karatun ta kasance yanda shi kansa mai karantawa zai iya ji idan babu abin da ya hana shi ji. *(Baĥâr-e-Sharî'at, juzu'i na 1, sashe na 4, shafi na 728)*

4. Ba lallai ba ne mai saurare ya ji karatun ayar da gangan, Sujjada ta na zama Wajibi ko da ya jiyo ayar ba da gangan ba. *(Al-Ĥidâyaĥ, juzu'i na 1, shafi na 78)*

5. Idan aka karanta ayar da irin sautin da za a ji, amma saboda hayaniya ko kurumci y ahana ya ji, sujjada ta zama Wajibi a gare shi. Sai dai idan lebbansa sun motsa amma ba a fitar da sautin ba, to sujjadar ba za ta zama Wâjib ba. *(Fatâwâ 'Âlamgîrî, uzu'i na 1, shafi na 132)*

6. Ba lallai ba ne sai an karanta dukan ayar sannan sujada ta ke zama Wajibi. Karanta kalmar ayar sujjada, da kalmar da ke gabanta ko bayanta, ya wadatar [domin ta zama Wâjibi].

*(Rad-dul-Muhtâr, vol. 2, p. 694)*

7. **Hanyar yin Sujjadaĥ Tilâwat:** Hanyar yin sujjada ta Sunnar Sujjadah Tilawat ita ce: Ka tashi tsaye ka ce: اَللّٰهُ اَكْبَر sannan sai kayi sujjadah (kana mai cewa اَللّٰهُ اَكْبَر) kuma ka maimaita cewa akalla so 3 : سُبْحٰنَ رَبِّيَ الْاَعْلٰي. Sannan kana me cewa اَللّٰهُ اَكْبَر, ka taso daga sujjadah. Sunna ce yin kabbara ma اَللّٰهُ اَكْبَرkafin sujjada da kuma idan an dawo daga sujjadah. Tsayuwa gabanin sujjada da tsayuwa bayan yin sujjada dukkanin su Mustahabbi ne. *(Durr-e-Mukhtâr, juzu'i na 2, shafi na 699)*

8. Ba ya wajaba ga wanda zai yi Sujjadaĥ Tilawat ya ɗaga hannuwansa yana cewa اَللّٰهُ اَكْبَر, ko karanta Tahiya (Attahiyyat) ko yin sallama. *(Tanvîr-ul-Absâr, juzu'i na 2, shafi na 700)*

9. Lokacin yin niyya ga Sujjadaĥ Tilâwat, ba lallai bane a danganta ta da takamaiman Aya, niyya gamammia tayin Sujjadaĥ Tilawat ta wadatar. *Durr-e-Mukhtâr, Rad-dul-Muhtâr, juzu'i na 2, shafi na 699)*

10. Idan aka karanta ayar sujjada a cikin sallah, ba wajibi bane gaggauta yin sujjadar. Duk da haka, yana da kyau a yi shi nan da nan. Idan mutum yana cikin alwala, jinkirta shi, abin kyema ne (Makruĥ Tanzi'i ne). *(Durr-e-Mukhtār, juzu'i na 2, shafi na 703)*

11. Idan ba zai yiwu a yi Sajdaĥ a wannan lokacin ba saboda wani dalili, Mustahabbi ne ga mai karatu da mai sauraro su karanta:

سَمِعْنَا وَ اَطَعْنَا ۗ غُفْرَانَكَ رَبَّنَا وَ اِلَيْكَ الْمَصِيْرُ ﴿۲۸۵﴾

*Mun ji kuma mun bi (mun yi ɗa'a), muna neman gafarar Ka, ya Ubangijin mu, zuwa a gare Ka (kaɗai) ne makoma take.*

*[Kanz-ul-Îmân (Traduction du Saint Coran)] (juzu'i na 3, Al-Baqaraĥ, aya ta 285)*

*(Rad-dul-Muhtâr, juzu'I na 2, shafi na 703)*

12. Idan kuma a majalissi (taro) aka karanta ayar sujjada ko aka saurare ta sau da yawa, sujjada daya kawai takes zama Wâjibi, koda kuwa mutane daban-daban sun ji. Haka nan idan mutum ya

karanta aya [sujjada], sannan ya ji wannan aya daga wurin wani, sujjada guda za ta zama Wajib a gare shi.

*(Durr-e-Mukhtâr, Rad-dul-Muhtâr, juzu'i na 2, shafi na 712)*

13. Abin kyema ne tare da haramci barin ayar sujjada a gefe yayin karanta surar gabaɗaya. Babu laifi a karanta ayar sujjada ita kaɗai, amma yana da kyau a karanta wasu ayoyin da suka gabace ta ko su ke baya da ita. *(Durr-e-Mukhtâr, juzu'i na 2, shafi na 717)*

## Domin biyan bukatu

14. Domin samun biyan buqata bisa aqidar Hanafiyya akwai ayoyi 14 na sujjada a cikin Alqur'ani mai girma, kuma idan aka karanta wadannan ayoyi 14 a Majlisi da wata manufa ta musamman, sannan aka yi sujjada, Allah عَزَّوَجَلَّ zai cika wannan manufar. Cewa mutum yayi sujjada bayan kowace Aya ko kuma yayi sujjada 14 a hade bayan ya karanta. Ayoyi 14.

*(Baĥâr-e-Sharî'at, juzu'i na 1, sashe na 4, shafi na 738)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب     صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Ayoyin 14 wanda ake sujudi a gurin su

| | |
|---|---|
| 1. | اِنَّ الَّذِيْنَ عِنْدَ رَبِّكَ لَا يَسْتَكْبِرُوْنَ عَنْ عِبَادَتِهٖ وَيُسَبِّحُوْنَهٗ وَلَهٗ يَسْجُدُوْنَ ﴿۲۰۶﴾ |

| | |
|---|---|
| | *(juzu'i na 9, Suratul-A'râf, aya ta 206)* |
| 2. | وَلِلّٰهِ یَسْجُدُ مَنْ فِی السَّمٰوٰتِ وَالْاَرْضِ طَوْعًا وَّ كَرْهًا وَّ ظِلٰلُهُمْ بِالْغُدُوِّ وَالْاٰصَالِ ۩ ﴿۱۵﴾ |
| | *(juzu'i na 13, Suratur-Ra'd, aya ta 15)* |
| 3. | وَلِلّٰهِ یَسْجُدُ مَا فِی السَّمٰوٰتِ وَمَا فِی الْاَرْضِ مِنْ دَآبَّةٍ وَّالْمَلٰٓىٕكَةُ وَهُمْ لَا یَسْتَكْبِرُوْنَ ﴿۴۹﴾ |
| | *(juzu'i na 14, Suratun-Nahl, aya ta 49)* |
| 4. | اِنَّ الَّذِیْنَ اُوْتُوا الْعِلْمَ مِنْ قَبْلِهٖۤ اِذَا یُتْلٰى عَلَیْهِمْ یَخِرُّوْنَ لِلْاَذْقَانِ سُجَّدًا ﴿۱۰۷﴾ وَّ یَقُوْلُوْنَ سُبْحٰنَ<br>رَبِّنَاۤ اِنْ كَانَ وَعْدُ رَبِّنَا لَمَفْعُوْلًا ﴿۱۰۸﴾ وَ یَخِرُّوْنَ لِلْاَذْقَانِ یَبْكُوْنَ وَ یَزِیْدُهُمْ خُشُوْعًا ۩ ﴿۱۰۹﴾ |
| | *(juzu'i na 15, Suratu Banî Isrâîl, aya ta 107 zuwa ta 109)* |
| 5. | اِذَا تُتْلٰى عَلَیْهِمْ اٰیٰتُ الرَّحْمٰنِ خَرُّوْا سُجَّدًا وَّ بُكِیًّا ۩ ﴿۵۸﴾ |
| | *(juzu'i na 16, Suratu Maryam, aya ta 58)* |
| 6. | اَلَمْ تَرَ اَنَّ اللّٰهَ یَسْجُدُ لَهٗ مَنْ فِی السَّمٰوٰتِ وَ مَنْ فِی الْاَرْضِ وَ الشَّمْسُ وَ الْقَمَرُ وَ النُّجُوْمُ وَ الْجِبَالُ وَ<br>الشَّجَرُ وَ الدَّوَآبُّ وَ كَثِیْرٌ مِّنَ النَّاسِؕ وَ كَثِیْرٌ حَقَّ عَلَیْهِ الْعَذَابُؕ وَ مَنْ یُّهِنِ اللّٰهُ فَمَا لَهٗ مِنْ<br>مُّكْرِمٍؕ اِنَّ اللّٰهَ یَفْعَلُ مَا یَشَآءُ ۩ ﴿۱۸﴾ |
| | *(juzu'i na 17, Suratul Hajj, aya ta 18)* |
| 7. | وَ اِذَا قِیْلَ لَهُمُ اسْجُدُوْا لِلرَّحْمٰنِ قَالُوْا وَ مَا الرَّحْمٰنُۗ اَنَسْجُدُ لِمَا تَاْمُرُنَا وَ زَادَهُمْ نُفُوْرًا ۩ ﴿۶۰﴾ |
| | *(juzu'i na 19, Suratul-Furqân, aya ta 60)* |



www.dawateislami.net

| | |
|---|---|
| 8. | أَلَّا يَسْجُدُوا لِلَّهِ الَّذِي يُخْرِجُ الْخَبْءَ فِي السَّمٰوٰتِ وَالْأَرْضِ وَيَعْلَمُ مَا تُخْفُونَ وَمَا تُعْلِنُونَ ﴿٢٥﴾ اللَّهُ<br>لَا إِلٰهَ إِلَّا هُوَ رَبُّ الْعَرْشِ الْعَظِيمِ ۩ ﴿٢٦﴾ |
| | *(juzu'i na 19, Suratun-Naml, aya ta 25 zuwa ta 26)* |
| 9. | إِنَّمَا يُؤْمِنُ بِآيٰتِنَا الَّذِينَ إِذَا ذُكِّرُوا بِهَا خَرُّوا سُجَّدًا وَسَبَّحُوا بِحَمْدِ رَبِّهِمْ وَهُمْ لَا يَسْتَكْبِرُونَ ۩ ﴿١٥﴾ |
| | *(juzu'i na 21, Suratus-Sajdaĥ, aya ta 15)* |
| 10. | فَاسْتَغْفَرَ رَبَّهُ وَخَرَّ رَاكِعًا وَأَنَابَ ۩ ﴿٢٤﴾ فَغَفَرْنَا لَهُ ذٰلِكَ ۖ وَإِنَّ لَهُ عِنْدَنَا لَزُلْفٰى وَحُسْنَ مَاٰبٍ ﴿٢٥﴾ |
| | *(juzu'i na 23, Suratu Sâd, aya ta 24 zuwa ta 25)* |
| 11. | وَمِنْ اٰيٰتِهِ اللَّيْلُ وَالنَّهَارُ وَالشَّمْسُ وَالْقَمَرُ ۚ لَا تَسْجُدُوا لِلشَّمْسِ وَلَا لِلْقَمَرِ وَاسْجُدُوا لِلَّهِ<br>الَّذِي خَلَقَهُنَّ إِنْ كُنْتُمْ إِيَّاهُ تَعْبُدُونَ ﴿٣٧﴾ فَإِنِ اسْتَكْبَرُوا فَالَّذِينَ عِنْدَ رَبِّكَ يُسَبِّحُونَ لَهُ<br>بِاللَّيْلِ وَالنَّهَارِ وَهُمْ لَا يَسْأَمُونَ ۩ ﴿٣٨﴾ |
| | *(juzu'i na 24, Suratu Hâ-Mîm As-Sajdaĥ, aya ta 37 zuwa ta 38)* |
| 12. | فَاسْجُدُوا لِلَّهِ وَاعْبُدُوا ۩ ﴿٦٢﴾ |
| | *(juzu'i na 27, Suratun-Najam, aya ta 62)* |
| 13. | فَمَا لَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٢٠﴾ وَإِذَا قُرِئَ عَلَيْهِمُ الْقُرْاٰنُ لَا يَسْجُدُونَ ۩ ﴿٢١﴾ |
| | *(juzu'i na 30, Suratul-Inshiqâq, aya ta 20 zuwa ta 21)* |
| 14. | وَاسْجُدْ وَاقْتَرِبْ ۩ ﴿١٩﴾ |
| | *(juzu'i na 30, Suratul-'Alaq, aya ta 19)* |

## Lu’a lu’an Madina 9 gameda taba Al-Qur’ani mai Girma

1. Idan mutum baya da tsarki (alwala) to ya wajaba ya yi alwala kafin ya taɓa AlQur'ani mai girma. *(Nûr-ul-Îdâh, shafi na 18)*

2. Idan mutum baya cikin alwala, ya halatta ya karanta AlQur'ani mai girma ya na mai kallo ba tare da ya taɓa shi ba.

3. Bai halalta ba yin taimama don taɓa AlQur’ani mai girma ko don yin Sajdaĥ Tilawat, ko kuma yin Sajdaĥ Shukr (sujjadar godiya), a lokacin da ruwa suna a kusa. *(Baĥâr-e-Sharî’at, juzu’I na 1, sashe na 2, shafi na 352)*

4. Haramun ne ga wanda wanka ya wajaba a kan shi (wankan tsarki) ya taɓa Alqur'ani mai girma. Wannan ya haɗa da gefe takarda, bango na AlQur'ani mai girma. Haka nan Haramun ne gare shi ya karanta Alqur'ani mai girma yana mai kallo ko karanta shi da ka, da rubuta aya, ko rubuta Ta'wiz [layya] na aya, ko taɓa irin wannan layya, ko taɓa ko sanya irin wannan zobe, wanda aka rubuta ayoyin Alqur’ani a kansa, misali zobe da aka rubuta yankakkun haruffa[2] [Huruful-Muqatta’at] a kansa. *(Baĥâr-e-Sharî’at, juzu’I na 1, shafi na 2, shafi na 326)*

5. Idan har Alqur'ani mai girma yana cikin jaka, ya halatta a taɓa jakar. Haka nan ya halatta a taɓa shi ta hanyar amfani da kyalle ko wani nau'in tufa da ba shi cikin jikin ku ko lake da’ AlQur'anin mai girma. Haramun ne ka taɓa Al-Qur'ani mai girma da hannun

---

[2] قٓ – طٰهٰ – يٰسٓ – كٓهٰيٰعٓصٓ – الٓمّٓ da sauran su. Ana kiran su yankakkun haruffa

rigarka ko gefen gyale (mayahi), ko da kusurwar gyale daya ta rataya a kafada ɗaya, ba za ka iya amfani da ɗayan kusurwar wannan gyale wajen taɓa Al-Qur'ani ba, saboda duka waɗannan ana ɗaukarsu a matsayin wani bangare ne na jikin ku ko a kan jikin ku, kamar yadda ake ganin bangon AlQur'ani mai girma a mallake a gare shi.

*(Durr-e-Mukhtâr, Rad-dul-Muhtâr, juzu’I na 1, shafi na 348)*

6. Dokokin da suka shafi karatun AlQur'ani mai girma da kuma taɓa shi, to hakan sun shafi fassara AlQur'ani mai girma zuwa Hausa, Farisanci ko da kowane irin harshe ma.

*(Baĥâr-e-Sharî’at, partie 2, p. 327)*

7. Ba ya halatta ga wanda bai yi alwala ba, ko kuma wanda waka ya wajaba a kansa, ya taɓa aya da aka rubuta a cikin littafi ko a jarida. Haka nan ba ya halatta a taba bayan takarda kai tsaye a bayan sashin da aka rubuta ayar.

8. Wanda bai yi alwala ba ko kuma wanda wanka ya wajaba a kansa ba ya halatta ya taɓa wani bangare na takarda wanda aya kawai aka rubuta, ba wani abu ba, wannan ya hada da taɓa gaba, baya, gefuna, da sauransu.

*Kalām-e-Pāk kay Maulā mujĥay ādāb sikĥlā day*
*Mujĥay Ka’baĥ dikĥā day Gumbad-e-Khazrā bĥī dikĥlā day*

*Yā Allah! Ka bani ikon koyon karatun wanan AlQur’ani mai girma*
*Ka nu namini Ka'aba, da Kubba nan koriya, ma su albarka*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Madani Bukata mahimmiya ga Mawallafa

9. Wannan roƙo ne Madani na gaskiya ga masu buga littattafan addini da jaridu na wata-wata da su guji buga ayoyi ko fassarar ayoyi a kowane bango ko gefe, na gaba ko bayan littattafai, ƙasidu, da sauransu. Domin kuwa ta hanyar ɗaukar littafin da taɓa shi, musulmi dayawa a rabkane suna taɓa ayoyin, ba tare da sun yi alwala ba.

   A kan haka, 'Allâmaĥ Maulânâ Al-Hâj Al-Ḥâfiz Al-Qârî Ash-Shâĥ Imâm Ahmad Razâ Khân رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه ya ce a shafi na 393 juzu'i na 23 na Fatâwa Razawîyyaĥ : "Buga ayoyi a kan takarda da aka naɗe da damshi ko dam na jaridu ko 'yan littattafai, ko a kati ko ambulan, yana haifar da rashin mutuntawa kuma yana haifar da Harâm. Saboda wa 'yan su abu ko wasu mutanen da ba su da 'alwala ko jahilci, ko kuma Kuffari (kafirai) wadanda a kodayaushe suke cikin najasa (wato ba tare da tsarki ba), wannan kuma haramun ne. Allah عَزَّوَجَلَّ ya na cewa:

لَا يَمَسُّهٗۤ اِلَّا الْمُطَهَّرُوْنَ ﴿۷۹﴾

*Babu mai shafa shi sai ma su tsarki (Alwala).*

*[Kanz-ul-Īmān (Fassarar AlQur'ani mai girma)]*

Ana iya ajesu a ƙasa don a hauda hatimi a saman su, ana iya yayyage su a jefar da su cikin shara, kuma wannan ayar da aka yi amfani da ita ba daidai ba, sakamakon aikin edita ne ko mawallafin."

*Menene bangaskiya (imani)? Na tambayi hankalina Hankalina*
*Ya amsa da cewa: Imani shine dukan girmamawa.*

سُبۡحٰنَ اللّٰـه عَزَّوَجَلَّ! Idan kun ga an buga ayar Alqur’ani mai girma a bangon littafi, ana buqatar ku, bayan kun yi kyakkyawar niyya, ku nuna wa mawallafin wannan nassin da aka ambata a sama ko ku aika masa da hoto ta hanyar wasiku [ko ta imel]. Da wannan ya kamata ku rubuta: “Bayan ganin ayar Al-Qur’ani mai girma a bangon littafinku mai suna [kaza], na rubuto muku da cewa ku daina buga ayoyi ko tafsirinsu a bangwoyen littattafa. , domin a kiyaye musulmi daga shafa su ba tare da sun yi alwala ba. جَزَاكَ اللّٰهُ خَيْرًا !

Idan shi mawallafin masoyin masana addinin musulnci ne اِنۡ شَـآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ zai albarkace ku da addu'o'insa, kuma zai bayyana aniyarsa ta yin taka tsantsan a kan irin wannan lamari a nan gaba.

*Maḥfūẓ Khudā rakĥnā sadā bay-adabaun say*
*Aur mujĥ say bĥī sarzad na kabĥī bay-adabī ĥo*

*Ya Allah! Ka nisanta ni daga ma su rashin ladabi ga AlQur’ani*
*Kada Kasa nayi rashin ladabi ga littafin Ka mai Girma.*

صَلُّوۡا عَلَى الۡحَبِيۡب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Lu’a lu’an Madina 4 gameda Fassara Al-Qur’ani mai Girma

1. Kada a yi tarjamar Alqur'ani mai girma ba tare da tafsiri ba [fashin baki]. Ga taqaitaccen sashe na Fatawar da A'lâ Hadrat Imâm Ahmad Razâ Khân رَحۡمَةُ اللّٰهِ عَلَيۡه ya rubata cewa: “Ba shi



www.dawateislami.net

yiwuwa a sami fahimta ta hanyar karanta tafsirin Alqur'ani mai girma ba tare da zurfafan ilimi ba. A hakikanin gaskiya akwai cutarwa fiye da alheri a cikin wannan hanyar.

idan har ku karanta tafsirin, dole ne ku yi hakan a karkashin jagorancin wasu masana, malaman addini cikakkun Ahlus Sunna." *(Fatâwâ Razawiyyaĥ – referencé, juzu'i na 23, shafi na 382)*

2. Don fahimtar Al-Qur'ani mai girma, ku sami kwafin fassarar da A'lâ Hadrat, mai rayar da Sunna, jagoran Tarîqa, malamin Shari'a, 'Allâmaĥ Maulânâ Al-Hâj Al-Hâfiz Al-Qârî Ash-Shaih Imâm Ahmad Razâ Khân رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه, Kanz-ul-Iman [Taskar Imani]", gami da sharhin sunan "Khazâin-'Irfān" wanda "Allâmaĥ Maulânâ Sayyid Na'îmuddîn Murâdâbâdî رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه" ya rubuta.

3. Ku yi aiki da "Neik Amaal"[3] ta hanyar karanta ayoyi 3 na Alqur'ani a kullum (Tare da fassarar da sharhi), اِنْ شَآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ za ku ga albarkar da kanku.

[3] A yankin Madani na DawateIslami, akwai Neik Amaal [Ayyukan Ibada] 72 ga 'yan'uwa maza a Musulunci da 63 ga 'yan'uwa mata a Musulunci, wanda aka tsara a cikin hanyar tambayoyi a cikin ɗan littafi don taimaka ma musulmi su yi rayuwa mai daɗi ta Musulunci. Don haka wanda suka samu damar aykata wa, su rika yin Tunani a kan rayuar su a kullum tare da cika akwatinan amsa' ga tambayoyi. Sannan a mayar da littafin zuwa ga [wakilin] DawateIslami na yanki su, a cikin kwanaki 10 na farkon kowane sabon watan Musulunci. Domin sanin cikakkiyar hanyar wannan manufa, ku sami ɗan littafin mai suna "Neik Amaal" a Maktaba-tul-Madînaĥ [sashe wallafe-wallafen Dawat-e-Islami]. Mafi yawan wallafe-wallafen Maktaba-tul-Madinah yana a saman yanar gizon: www.dawateislami.net don saukewa kyauta.

4. A bisa tsare-tsare na Dawat-e-Islami, kowane masallaci an dauke shi a matsayin Zaylī Halqaĥ (wani reshe ne). A cikin kowace Zaylī Halqaĥ, manufar ita ce a kafa Madani Halqaĥ (da'irar nazari) a kowace rana bayan sallar asuba don karanta da sauraren ayoyi 3 na Alqur'ani mai girma tare da tafsirin Kanz-ul-Iman da tafsirin Khazâin-ul-Irfān/Nur-ul-Irfān. Idan za ta yiwu, duk 'yan'uwa Musulmi su yi ƙoƙari su sami albarka ta hanyar shiga Madani Halqaĥ.

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Lu'a lu'an Madina 2 a kan binnewa ko nitsawa cikin ruwa na shafukkan Alqur'ani

1. Idan rubutun Alqur'ani mai girma ya tsufa ta yadda ba za a iya karanta shi ba kuma akwai yuwuwar rubewa shafukan a hankali, ko kuma su lalace, sai a nade shi da tsaftataccen kyalle. Kuma akan binne shine a wuri mai tsaro. Don yin haka sai a yi Lahad (wani nau'in kabari) (bayan an tona rami a yi budi a bangon da ke fuskantar alkibla, wanda ya kai girman da ya kunshi dukkan shafuffuka masu tsarki) don kada kasa ta fado sama. Ko kuma, bayan sanya shi a cikin rami, sai sanya katako a kan shi don mafaka, kada datti ya fada a kansa. Idan rubutun kur'ani mai girma ya tsufa, kada a kona shi.

*(Baĥâr-e-Sharî'at, sashe na 16, shafi na 138)*

2. Bai kamata a sanya shafuffukan Alqur'ani mai tsarki a cikin ruwa mara zurfi ba, ko kuma a cikin wani kogi ko rafi wanda bai da zurfi, saboda hakan na sa su shawagi a gaɓar teku da kuma haifar da rashin mutuntawa sosai. Hanyar sanya su a cikin tekun ita ce a fara sanya su a cikin jakar da ba komai, da dutse mai nauyi, sannan a yi 'yan fudodi a cikin jakar ta yadda ruwa zai shiga cikinta nan da nan sai a nutse sa zuwa kasan tekun. Idan ruwa bai shiga cikin jakar ba, wani lokaci yakan yi ta yawo har tsawon kilometa masu yawa kuma ya kai ga gaci.

   A cikin kwadayin samun jakar, sai ya faru cewa mutane marasa wayewa, ko ma Kafure, suna tattara shafukan da ake mutuntawa a bakin tekun. Lokacin da irin waɗannan munanan ayyuka na rashin mutuntawa suke faruwa, zuciyar mai ibada takan fara rawa da jin irin waɗannan abubuwan.

Don tabbatar da cewa jakar ta isa zurfin teku, ana iya samun taimako daga wani jirgin ruwa na musulmi, amma dolene a tuna cewa dolene fa a yi la'akari a kowane hali.

*Mayn adab Quran kā ĥar ḥāl mayn kartā raĥūn*
*Ĥar gĥaŕī ay mayray Maulā Tujĥ say mayn ḋartā raĥūn*

*Ka sa ni a ko da yaushe ina mai girmama Alqur'ani*
*Ya Allah! don tsoran ka ne ni ke makarkata ko da yaushe*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد



www.dawateislami.net

## Lu'a lu'an Madina 8 daban-daban

1. Hanya mai kyau ita ce adana Alqur'ani a cikin akwati ko a cikin jaka. Musulmi sun kasance suna yin haka tun zamanin Sahabbai da Taabi'in رَضِیَ اللّٰہُ عَنۡہُمۡ اَجۡمَعِیۡن.

   *(Bahâr-e-Sharî'at, sashe na 12, safi na 139)*

2. Ɗaya daga cikin kyawawan ɗabi'un Alkur'ani mai girma shi ne ka nisanci juya masa baya, da mike kafafun ka zuwa gare shi, da ɗaga kafafun ka sama da shi, sannan su kasance a saman inda yake aje. *(ibid)*

3. Ilmi 3 na Lughât [harshe], Nahw [nahawu: syntax na Larabci], da Sarfu [morphology] duk daidai suke a matsayi. Ya halatta a sanya wani littafi na waɗannan ilimomi sama da wani. A kan waɗannan ana iya ɗora littafan Ilmul Kalami, a kan waɗannan ana iya ɗora littafan Fiqhu, kuma a kan wadannan ana iya ɗora littafan Hadisi da addu'o'in da aka ambata a cikin Alkur'ani da Hadisi sannan.

4. A kan haka, za mu iya sanya littattafai na Tafsiri, kuma a karshe, a kan dukan wannan, za mu iya sanya Mai Tsarki Alqur'ani. Kada ku sanya tufafi a cikin akwati da aka sanya Alkur'ani mai girma. *(Fatâwâ 'Âlamgîrî, juzu'i na 5, shafi na 323-324)*

5. Idan mutum ya ajiye kwafin Alkur'ani mai girma a gidansa da nufin samun albarka da alheri, amma ba ya karanta shi, ba zai kasance mai zunubi ba. Hasali ma wannan niyya nasa ta zama hanyar samun lada a gare shi. *(Fatâwâ Qâdî Khân, juzu'i na 2, shafi na 378)*

6. Idan Alqur'ani mai girma ya fado daga hannun wani ba da gangan ba ko kuma daga abin da yake rike da shi, to babu laifi a kansa, kuma ba bu wata Kaffara a kansa.

7. Idan wani مَعَاذَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ ya jefa Alqur'ani a kasa da niyyar wulaqanta shi, ko kuma ya ɗora qafafunsa akan Alqur'ani mai girma da nufin wulaqanta shi, ya kafurta.

8. Maganar da aka yi ta hanyar kalmomi na alwashi ko rantsuwa yayin da ake rike da Al-Qur'ani mai girma a hannaye, ko sanya hannu a kan Al-Qur'ani mai girma, ana ɗaukar shi a matsayin kakkausan (rantsuwa). Duk da haka, idan mutum ya faɗi wani abu ba tare da faɗi takamaiman kalmomi na alwashi ba yayin da yake riƙe da Alqur'ani mai girma a hannunsa ko kuma ya sanya hannunsa a kan Al-Qur'ani mai girma, a cikin haka ba zai kasance wa ba (rantsuwa) kuma babu Kaffara a gare shi. *(Fatâwâ Razawiyyaĥ – référencé, juzu'i na 13, shafi na 574-575)*

9. Ko da akwai Alqur'ani da yawa da ake ajiyewa a masallaci, kuma ba duka ake amfani da su ba, wa ɗansun ana anfani da su, to haramunne a fansar da su don yin anfani da kuɗin a cikin lamurran Masallacin. Duk da haka, ana iya rarraba waɗannan Alqur'anan don sanyawa a wasu Masallatai da Makarantu. *(Fatâwâ Razawiyyaĥ – referencé, juzu'I na 16, shafi na 164)*

*Ĥar roz mayn Quran pařĥūn kāsh Khudāyā*
*Allah! Tilāwat mayn mayray dil ko lagā day*

*Ya Allah! Ya Allah! Ka sa karatun ya kasance cikin al'amurana na yau da kullun!*
*In dinga karanta Al-Qur'ani da zuciya ɗaya, ina me cike da farin ciki!*

## Lu'a lu'an Madina 5 game da aika lada ga mamaci (Îsâl-e-Sawâb)

1. Annabi Masoyin mu kuma mai albarka صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce Hālin da mamaci yake a cikin kabarinsa kamar wanda ya nutse ne, cikin tashin hankali, yana jiran addu'ar mahaifinsa, mahaifiyarsa, dan uwansa ko abokinsa. Idan addu'ar wani ta zo masa, sai ya ɗauke ta fiye da duniya da abin da ke cikinta. Allah عَزَّوَجَلَّ yana bayar da ladan da 'yan uwa masu rai suke bayarwa ga mamaci kamar tsaunuka. Kyautar masu rai ga mamacin ta kunshi neman gafarar su." *(Shu'ab-ul-Îmân, uzu'i na 6, shafi na 203, Hadisi na 7905)*

2. Ya zo a cikin Tabarani cewa: "Idan wani ya aika da Sawab [lada] na aikin alheri ga mamaci, sai mala'ikan Jibrîl عَلَيْهِ السَّلَام ya sanya ladan kan tire mai haskawa ya tsaya yana ɗauke da ita kusa da kabari ya ce: "Ya ma'abocin kabari! Masoyanka sun aiko da kyauta, karɓa." Jin haka sai ya yi farin ciki, yayin da maƙwabtansa (maƙwabtansa matattu da ke cikin kaburbura) su ku wa na baƙin ciki da rashin samun wanda za su turo masu da kyata." *(Al-Mu'jam-ul-Awsat, juzu'I na 5, shafi na 37, Hadisi na 6504)*

*Qabr mayn āĥ! Għup andĥayrā ĥay*
*Fazl say karday chāndnā Yā Rab*

*Kaico! kabari mai bantsoro yafi dare duhu.*
*Ya Allah! don rahamar Ka, Ka haskaka shi da haskenKa.*



www.dawateislami.net

3. Baya ga İsâl-e-Shawab na karatun Al-Qur'ani mai girma, mutum yana iya yin Ishal-e-Shawab na duk wani aikin alheri na farilla, Wâjib, Sounnaĥ, nafila, na sallah, na azumi, na zakka, na Hajji, da furta magana ko Dars, tafiya zuwa Madani Qafilaĥ, aiki bisa ga Neik Amaal, shiga cikin kira zuwa ga adalci, nazarin littafin addini ko ƙoƙarin mutum na ayyukan Madani, da sauransu.

## Hanyar aika lada ga mamaci (Îsâl-e-Šawâb)

4. Hanyar İsâl-e-Shaawâbl’Isal-e-Shawab ba abu ne mai wahala ba, ya isan muku kawai ku niyya a cikin zuciya cewa: “Ya Allah عَزَّوَجَلَّ! Ka ba da ladan Al-Qur'ani mai girma da na karanta (ko ladan wannan aikin alheri nawa) ga mahaifiyata marigayiya.” اِنْ شَآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ laɗan zai isa gare ta.

## Hanyar karatun Fâtihaĥ

Hanyar karatun Fatiha wadda ta zama ruwan dare a tsakanin musulmi a yau, musamman akan walima, yana da kyau sosai. Kamar yadda ake yin hakane don aika ladan karatu da sauransu ga mamaci. Kuma za a iya yin su a lokaci guda. Ku sanya duk abincin da aka shirya don İsâl-Shawab a gabanku (ko kuma wani yanki na kowane kayan dafuwar), da kopin ruwa. Sai ku karanta اَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ, sannan ku karanta Suratul Kafirûn sau ɗaya.

بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ

---

قُلْ يٰۤاَيُّهَا الْكٰفِرُوْنَ ۝١ لَاۤ اَعْبُدُ مَا تَعْبُدُوْنَ ۝٢ وَلَاۤ اَنْتُمْ
عٰبِدُوْنَ مَاۤ اَعْبُدُ ۝٣ وَلَاۤ اَنَا عَابِدٌ مَّا عَبَدْتُّمْ ۝٤ وَلَاۤ اَنْتُمْ عٰبِدُوْنَ
مَاۤ اَعْبُدُ ۝٥ لَكُمْ دِيْنُكُمْ وَلِيَ دِيْنِ ۝٦

---

Ku karanta Suratul-Ikhlâs sau 3:

بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ

---

قُلْ هُوَ اللّٰهُ اَحَدٌ ۝١ اَللّٰهُ الصَّمَدُ ۝٢ لَمْ يَلِدْ ۙ وَلَمْ يُوْلَدْ ۝٣
وَلَمْ يَكُنْ لَّهٗ كُفُوًا اَحَدٌ ۝٤

---

Ku karanta Surat-Al-Falaq sau guda:

بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ

---



www.dawateislami.net

قُلْ اَعُوْذُ بِرَبِّ الْفَلَقِ ۙ﴿۱﴾ مِنْ شَرِّ مَا خَلَقَ ۙ﴿۲﴾ وَ مِنْ شَرِّ غَاسِقٍ اِذَا وَقَبَ ۙ﴿۳﴾
وَ مِنْ شَرِّ النَّفّٰثٰتِ فِی الْعُقَدِ ۙ﴿۴﴾ وَ مِنْ شَرِّ حَاسِدٍ اِذَا حَسَدَ ﴿۵﴾

Ku karanta Surat-Al-Nâs sau guda:

بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِیْمِ

قُلْ اَعُوْذُ بِرَبِّ النَّاسِ ۙ﴿۱﴾ مَلِكِ النَّاسِ ۙ﴿۲﴾ اِلٰهِ النَّاسِ ۙ﴿۳﴾ مِنْ شَرِّ
الْوَسْوَاسِ ۬ۙ الْخَنَّاسِ ۪ۙ﴿۴﴾ الَّذِیْ یُوَسْوِسُ فِیْ صُدُوْرِ النَّاسِ ۙ﴿۵﴾ مِنَ
الْجِنَّةِ وَ النَّاسِ ﴿۶﴾

Ku karanta Surat-Al-Fâtihaĥ sau guda:

بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِیْمِ

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِیْنَ ۙ﴿۱﴾ الرَّحْمٰنِ الرَّحِیْمِ ۙ﴿۲﴾ مٰلِكِ یَوْمِ
الدِّیْنِ ؕ﴿۳﴾ اِیَّاكَ نَعْبُدُ وَ اِیَّاكَ نَسْتَعِیْنُ ؕ﴿۴﴾ اِهْدِنَا الصِّرَاطَ
الْمُسْتَقِیْمَ ۙ﴿۵﴾ صِرَاطَ الَّذِیْنَ اَنْعَمْتَ عَلَیْهِمْ ۬ۙ غَیْرِ الْمَغْضُوْبِ

عَلَيْهِمْ وَلَا الضَّآلِّيْنَ ۝٧

Ku karanta sau guda-guda wadannan ayoyin masu zuwa:

بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ

الٓمّٓ ۝١ ذٰلِكَ الْكِتٰبُ لَا رَيْبَ ۛۚ فِيْهِ ۛۚ هُدًى لِّلْمُتَّقِيْنَ ۝٢ الَّذِيْنَ يُؤْ
مِنُوْنَ بِالْغَيْبِ وَيُقِيْمُوْنَ الصَّلٰوةَ وَمِمَّا رَزَقْنٰهُمْ يُنْفِقُوْنَ ۝٣ وَالَّذِيْنَ
يُؤْمِنُوْنَ بِمَآ اُنْزِلَ اِلَيْكَ وَمَآ اُنْزِلَ مِنْ قَبْلِكَ ۚ وَبِالْاٰخِرَةِ هُمْ يُوْ
قِنُوْنَ ۝٤ اُولٰٓئِكَ عَلٰى هُدًى مِّنْ رَّبِّهِمْ ۗ وَاُولٰٓئِكَ هُمُ الْمُفْلِحُوْنَ ۝٥

Sanan sai ku karanta ayoyinnan guda biyar masu zuwa:

| | |
|---|---|
| 1. | وَاِلٰهُكُمْ اِلٰهٌ وَّاحِدٌ ۚ لَآ اِلٰهَ اِلَّا هُوَ الرَّحْمٰنُ الرَّحِيْمُ ۝١٦٣ |
| | *(juzu’i na 2, Suratul-Baqaraĥ, aya ta 163)* |
| 2. | اِنَّ رَحْمَتَ اللّٰهِ قَرِيْبٌ مِّنَ الْمُحْسِنِيْنَ ۝٥٦ |

| | |
|---|---|
| | *(Juzu'i na 8, Suratul-A'râfi, aya ta 56)* |
| 3. | وَمَآ اَرْسَلْنٰكَ اِلَّا رَحْمَةً لِّلْعٰلَمِيْنَ ﴿۱۰۷﴾ |
| | *(Juzu'i na 17, Suratul-Anbiya'i, aya ta 107)* |
| 4. | مَا كَانَ مُحَمَّدٌ اَبَآ اَحَدٍ مِّنْ رِّجَالِكُمْ وَلٰكِنْ رَّسُوْلَ اللّٰهِ وَخَاتَمَ النَّبِيّٖنَ ؕ وَكَانَ اللّٰهُ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيْمًا ﴿۴۰﴾ |
| | *(Juzu'i na 22, Surate Al-Ahzâbi, aya ta 40)* |
| 5. | اِنَّ اللّٰهَ وَمَلٰٓئِكَتَهٗ يُصَلُّوْنَ عَلَى النَّبِيِّ ؕ يٰٓاَيُّهَا الَّذِيْنَ اٰمَنُوْا صَلُّوْا عَلَيْهِ وَسَلِّمُوْا تَسْلِيْمًا ﴿۵۶﴾ |
| | *(Juzu'i na 22, Suratul-Ahzâbi, aya ta 56)* |

Yanzu, kuyi salâti ga-An-Nabî ﷺ :

صَلَّى اللّٰهُ عَلَى النَّبِيِّ الْاُمِّيِّ وَاٰلِهٖ صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ
صَلٰوةً وَّسَلَامًا عَلَيْكَ يَارَسُوْلَ اللّٰهِ

Bayan haka, ku karanta :

سُبْحٰنَ رَبِّكَ رَبِّ الْعِزَّةِ عَمَّا يَصِفُوْنَ ﴿۱۸۰﴾
وَسَلٰمٌ عَلَى الْمُرْسَلِيْنَ ﴿۱۸۱﴾ وَالْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ ﴿۱۸۲﴾

*(Juzu’i na 23, Souratus-Sâffi, aya ta 180 zuwa ta 182)*

Yanzu mai yin Fatiha dole ne ya ɗaga hannuwansa ya ce: "Al-Fatiha" da babbar murya. Duk wadanda suke wurin sai su karanta suratu Fatiha da karamar murya, sannan mai yin Fatiha sai ya yi shela kamar haka: “Ku ba ni ladan abin da ku karanta”. Duk wanda ke wurin sai ya amsa da cewa, “Mun ba ku.” To, duk wanda ya yi Fatiha dole ne ya yi Issal-e-Shawab (bada ladan).

## Hanyar yin addou'a ta sadaka ga marigaya [Îsâl-e-Šawâb]

Ya Allah عَزَّوَجَلَّ! Ka ba mu ladan abin da aka karanta (idan an tanadar da abinci da sauransu) to sai a kara da cewa: da ladan abincin da aka tanadar da duk wani aiki da muka yi har izuwa yau, ba daidai da ayyukanmu na ajizai ba, amma daidai da Rahamar Ka marar iyaka, Ka isar da wannan lada (da sunayammu) a farfajiyar gidan masoyin Ka Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Ta hanyar Annabin Ka masoyin Ka صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, Ka isar da lada ga sauran Annabawa عَلَيْهِمُ السَّلَام, da dukkan sahabbai masu albarka رَضِىَ اللهُ عَنْهُم, da waliyyai masu daraja. رَحِمَهُمُ الله. Ta hanyar Annabin Ka masoyin Kaصَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ka isarlada ga duk wani musulmi dan Adam da aljani da aka haifa tun daga zuwan Sayyiduna Adam عَلٰى نَبِيِّنَا وَعَلَيْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام da duk wanda za a haifa har zuwa ranar sakamako.

A yayin wannan addu'a, kuma a ambaci sunayen waliyyai da ya kamata a ba su ladan musamman. Haka nan kuma, ku bayar da ladan ga iyayenku, danginku da Murshid (shehin ku). (Marigayin da aka ambaci sunayensa a lokacin kiran ya gamsar). Sannan ku kamala addu’ar kamar yadda aka saba.



www.dawateislami.net

(Idan an ajiye a gabanku kadan daga kowane nau'in kayan abinci da kopin ruwa, sai a sake haɗa shi da sauran abinci da ruwa).

*Šawāb a'māl kā Tū mayray puĥanchā sārī Ummat ko*
*Mujĥay bĥī bakhsh Yā Rab bakhsh un kī piyārī Ummat ko*

*Ka aika da ladan ayyukana ga daukacin al'ummah.*
*Ka gafarta wa dukkan al'ummar Masoyin mu.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Lu'a lu'an Madina 17 dangane da Sunna ɗarma Rawani

Da farko dai, ga hadissai guda 6 na masoyin mu Al-Mustafa ﷺ

1. Raka'a 2 na sallah da aka yi sanye da Rawani sun fi raka'a 70 ba tare da sanye da Rawani ba. *(Al-Firdaus bima'soor-il-Khitaab, juzu'i 2, shafi na 265, Hadisi na 3233)*

2. Sanya Rawani a kan hula shi ne bambancin mu da mushrikai. Domin kowane ginshiƙi na Rawani da musulmi ya lulluɓe kansa, to yana da Nur ɗaya [haske] a kansa, a ranar sakamako. *(Al-Jaami'-us-Sagheer, shafi na 353, Hadisi na 5725)*

3. Babu shakka, Allah عَزَّوَجَلَّ da Mala'ikunsa suna yin Salati a ranar Juma'a ga waɗanda suka sanya Rawani. *(Al-Firdaus bima'soor-il-Khitaab, juzu'I na 1, shafi na 147, Hadisi na 529)*

4. Yin salla ana sanya da Rawani ana samun lada 10 000.

*(Al-Firdaus bima'soor-il-Khitaab, juzu'I na 2, shafi na 406, Hadisi na 3805; Fatâwâ Razawiyyah, juzu'I na 6, shafi na 220)*

5. Sallar Juma'ah daya da aka yi sanye da Rawani tana daidai da salloli 70 ba tare da an sanya Rawani ba.

*(Tareekh-e-Madinah Dimashq li Ibn 'Asaakir, juzu'i na 37, shafi na 355)*

6. "Rawanin kambin Larabawa ne. Saboda haka ku yi riko da rawani. Duk wanda ya sa rawani, darajarshi ta na karuwa (a kowane naɗi da ya lullube kanshi)."

*(Jam'-ul-Jawaami', juzu'I na 5, shafi na 202, Hadisi na 14536)*

7. Ya zo a cikin littafi mai shafuka 312 mai suna "Baĥâr-e-Shari'at", wanda sashen buga littattafai na Dawat-e-Islami, Maktaba-tul-Madînaĥ ya buga, a shafi na 303, sashe na 16: "Ku ɗaure Rawani alhali kuna a tsaye, da sanya wando [ƙananan tufa] a zaune. Duk wanda ya aikata sabanin haka (wato ya daure Rawani a zaune, kuma ya sanya wando a tsaye), irin wannan cuta da ba ta da magani za ta same shi."

8. Ya fi dacewa a naɗin farko na Rawani, a ninka shi zuwa gefen dama na kai. *(Fatāwā Razawiyyaĥ, juzu'I na 22, shafi na 199)*

9. Shimlaĥ (wato jelar Rawani da ba a lulluɓe da ita ba) na Masoyin mu kuma Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya kasance yana rataya ta (a bayan bayansa mai albarka), wani lokaci a gefen dama, wani lokacin kuma akwai Shimla'i biyu tsakanin kafaɗunsa masu

albarka. rataya Shimlaĥ a gefen hagu ya sa saɓa wa Sunna. *(Ashi'a-tul-Lam'aat, juzu'i na 3, shafi na 582)*

10. Faɗin Shimlaĥ (jelar Rawani) dole ne ya zama aƙalla daidai da faɗin yatsu huɗu, kuma tsawonsa aƙalla har zuwa tsakiyar baya, wato kusan tsawon zira'i guda. *(Fatâwâ Razawiyyaĥ, juzu'i na 22, shafi na 182)*

11. Ku naɗa Rawanin yayin da ku ke tsaye ku na fuskantar alƙibla. *(Kashf-ul-Iltibâs fis-Tihbâb-il-Libâs lish-Shaykh 'Abdul Haq Diĥlvî, shafi na 38)*

12. Idan ku nada babban tufa da za ku iya samar da isassun naɗi da za su rufe kanku gaba ɗaya, za a ɗauke ta a matsayin Rawani.

13. Abin kyemane (Makaruh) a ɗaure kai da karamar tufa wanda ba za a iya yin ninki fiye da ɗaya ko biyu kawai. *(Fatâwâ Razawiyyaĥ – référencé, juzu'i na 7, shafi na 299)*

14. Idan za a cire rawani saboda larura, kuma a na da niyyar sake ɗaure shi da ga baya, za a shafe zunubi ta hanyar kwance kowane ninki. *(Fatâwâ Razawiyyaĥ, juzu'i na 6, shafi na 214)*

15. 'Allâma Shaikh 'Abdul Haq Muhaddiš Diĥlvî عَلَيْهِ رَحْمَةُ اللّٰهِ الْقَوِى ya ce: "Rawanin babban masoyin mu Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya kasance fari ne, wani lokaci baki wanibi kore." *(Kashf-ul-Iltibâs fis-Tihbâb-il-Libâs, shafi na 38)*

16-17. Sunnan Imama ita ce: kada ya kasance tsawonsa ya wuce mita 2½, kuma kada ya wuce mita 6, (17) kuma a daure shi da siffar kubba. *(Fatâwâ Razawiyyaĥ, juzu'i na 22, shafi na 186)*



www.dawateislami.net

اَلحَمۡدُ لِلّٰه عَزَّوَجَلَّ! Babban masoyin mu Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم wanda ya ke akwance kasan kubba nan koriya, Rahama ga halittu صَلَّى اللهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya na ƙawata kansa mai haske da Rawani kore mai albarka, kuma [Don haka nema] Dawat-e-Islami ta sanya koren Rawani alamar ta. Wani irin jan hankali koren rawani keda shi! Kubba mai haske da haskakawa bisa kabari mai albarka na Mai Makka da Madina, Masoyinmu kuma Annabin mu صَلَّى اللهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ita ma koriya ce! Kuma dole ne mabiyan Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم su sanya Rawani kore, domin su yi riqo kawunan su da launin kore su na kyalli. Haka kuma, koren bai kamata ya yi duhu sosai ba, sai dai ya kasance yana da kyau da haske ta yadda ko a cikin duhun dare ana iya ganin launinsa mai kyalli da haskakawa ta hanyar albarkar ƙeƙƙawar kubba Koriya.

*Naĥīn ĥay chānd sūraj kī Madīnay ko koī ḥājat*
*Waĥān din rāt un kā sabz gumbad jagmagātā ĥay*

*Madîna ba ta bukar wata, da rana, ko hasken su*
*Ita ta haskaka ne da hasken Kubba nan koriya dare da rana!*

صَلُّوۡا عَلَى الۡحَبِيۡب      صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Ku ba wa wani ɗan littafin nan bayan karanta shi

Za ku sami lada ta hanyar rarraba litattafai da Maktaba-tul-Madina ta buga da littattafan da ke ɗauke da Lu'a lu'an Madina a lokacin bukukuwan aure, jana'izar, Ijtima 'aat, munasabobi, na Mīlād. Maukibi (jerin gwano), da sauransu. Ku al'adatu da' adana 'yan littattafai a cikin kantinan ku don ba abokan cinikin ku da niyyar ribantar lada. Ku aiko da littafi ko kasida mai dauke da gyambon madani akalla guda daya ga duk wani gida da ke unguwarku tare da taimakon yara ko samarin da suka kai jarida, a kara zage damtse wajen isar da kira zuwa ga samun lada mai girma.

## Transliteration Chart

| | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|
| ء | A/a | ڑ | Ř/ř | ل | L/l |
| ا | A/a | ز | Z/z | م | M/m |
| ب | B/b | ژ | X/x | ن | N/n |
| پ | P/p | س | S/s | و | V/v, W/w |
| ت | T/t | ش | Sh/sh | | |
| ٹ | Ṫ/ṫ | ص | Ṣ/ṣ | ۃ/ ہ / ھ | Ĥ/ĥ |
| ث | Š/š | ض | Ḍ/ḍ | ی | Y/y |
| ج | J/j | ط | Ṭ/ṭ | ے | Y/y |
| چ | Ch | ظ | Ẓ/ẓ | ◌َ | A/a |
| ح | Ḥ/ḥ | ع | ‘ | ◌ُ | U/u |
| خ | Kh/kh | غ | Gh/gh | ◌ِ | I/i |
| د | D/d | ف | F/f | و مدّہ | Ū/ū |
| ڈ | Ḋ/ḋ | ق | Q/q | ی مدّہ | Ī/ī |
| ذ | Ż/ż | ك | K/k | ا مدّہ | Ā/ā |
| ر | R/r | گ | G/g | | |


اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ وَالصَّلٰوةُ وَالسَّلَامُ عَلٰى سَيِّدِ الْمُرْسَلِيْنَ اَمَّا بَعْدُ فَاَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ ؕ بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ ؕ

## BLOSSOMING OF SUNNAH

By the grace of Allah عَزَّوَجَلَّ, Sunnahs are abundantly learnt and taught in the Madani environment of Dawat-e-Islami, a global and non-political movement for the preaching of Quran and Sunnah. It is a Madani request that you spend the whole night in the weekly Sunnah-Inspiring Ijtima', taking place after Salat-ul-Maghrib every Thursday in your city, for the pleasure of Allah عَزَّوَجَلَّ with good intentions. With the intention of gaining reward, make it a part of your routine to travel in Sunnah-Inspiring Madani Qafilahs with the devotees of Rasul, to fill out the Madani In'amat booklet every day practicing Fikr-e-Madinah and to submit it to the relevant responsible Islamic brother of your locality within the first ten days of every Islamic month. Through the blessings of this, you will develop a mindset and a yearning to adopt Sunnahs, to have hatred for sins and to protect your faith, اِنْ شَآءَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ.

Every Islamic brother should develop the Madani mindset that **'I must strive to reform myself and people of the entire world, اِنْ شَآءَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ'**

In order to reform ourselves, we must act upon Madani In'amat and to strive to reform people of the entire world we must travel with Madani Qafilahs, اِنْ شَآءَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ.








ISBN 978-969-631-228-4
0101136
MC 1266

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagaran
Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan.
UAN: +92 21 111 25 26 92 | Ext: 1262
Web: www.dawateislami.net | E-mail: translation@dawateislami.net